# Amshi A Cikin Amshi: Wani Salon Amshi A Wasu Waqoqin Zamani

**Muhammad Abdul-Qadeer**
*Sashen Nazarin Harshen Hausa,*
*Kwalejin Koyon Shari'a Da Nazarin Addinin Musulunci, Nguru, Jihar Yobe*
*08065571789; Sawaba40@gmail.com*

Da

**Ibrahim Lamido**
*Sashen Koyar da Harsuna, Jami'ar Tarayya ta Kashere*
*07060777144; lamidoibrahim52@gmail.com*

**Tsakure**
Wannan takarda ta yi nazarin wani irin salo na amshi da aka fi sani da suna cafiya a wasu waqoqin Sitidiyo na Hausa. Nau'i ne na amshi dayake zuwa a qarshen kowane layi na xan waqa ban da layin qarshe. Takardar ta yi magana a kan ma'anar cafiya da nau'o'inta a waqoqin Sitidyo. Takardar ta gano mawaqan Hausa suna amfani da tsari daban-daban wajen qulla cafiya a waqoqin nasu. Binciken ya gwada yadda waoqin Hausa na Sitityo suke amfani da wani irin nau'i na amshi da ya sha bamban da na makaxan gargajiya. An duba bugaggun littatafai da kundayen bincike da maqalu a xakunan karatu da faya-fayen CD da na'urar naxan maganganu wajen tattara muhimman bayanai da wannan bincike yake buqata.
***Kalmomin fannu**: Cafiya, Amshi, Salo, Waqoqin Zamani, Karveveniya*

**Abstract**
This paper discusses the new style of choral response which is found in some Hausa modern poems called "cafiya". Unlike the one we know, which comes at the end of every stanza of a poem. This kind of choral response usually comes at the end of a line of every stanza; excluding the last line that regular refrain follows. Therefore, the paper contains the meaning of the word "cafiya" (new style of choral response), its types and importance in Hausa modern poems.Moreover, The paper discovers three types of new style of choral response and importance of it. The researcher used library materials that include: text books, theses, journals, papers, ICT etc as a method of data collection. An interview is also conducted.
**Keywords**: *Cafiya, Amshi, Salo, Waqoqin Zamani, Karveveniya*

## Gabatarwa

A bisa ma'ana ta harshe an bayyana ma'anar amshi da cewa: "Wani sashi ne na waqa da yaran mawaqa ke yawan maimatawa (qamusun Hausa, 2006:17). A fagen nazari kuwa, amshi (Qarvi) shi ne iyar da wata magana ko maimaita ta ko yi mata xoriya (Gusau, 2008:454). Masana adabi sun kasa 'yan amshi gida uku: 'yan amshin Shata da 'yan karvi da 'yan karveveniya. Wasu kuwa na ganin ba amshi ya dace a kasa gida uku ba, amshin kansa ya dace a kasa gida uku: wato amshi da karvi da karveveniya (Bunza, 2009:198 da 302). Waqoqin Hausa na zamani kuwa, waqoqi ne waxanda suka wanzu a sakamakon iya rubutu da karatu na Ajami da na Boko da Hausawa suka yi, sannan bisa yawanci ake shirya su a rubuce a samar da rauji da kixa, a kuma fitar da rerawa a sitidiyo (Gusau, 2014:13).

Ayyuka da dama sun gabata a kan nazarce-nazarce waxanda suka shafi waqoqi musamman na baka kamar su: bello (1976), Xangambo (1981), Gusau (1985), Gusau (2001), Schuh (2002) da sauransu. Wannan maqala dai ta yi tsokaci ne a kan wani salon

amshi da akan samu a wasu waqoqin zamani da ake yi wa laqabi da cafiya. Shi irin wannan amshi ba kamar irin amshin da aka saba ji ba ne, wanda yakan zo a qarshen xiyan waqa ko baiti. Shi irin wannan amshi akan yi shi ne a qarshen kowane xango na baiti, amma ban da xango na qarshen baiti wanda babban amshi yakan biyo bayansa. Don haka maqalar an kawo ma'anar cafiya da nau'o'in da yanaye-yanayenta kana da muhimmancinta.

## Ma'anar Cafiya

Cafiya ita ce, kame abin da ya faxo ko aka jefo (kamusun Hausa, 2006:19). Ta fuskar mawaqan zamani wannan kalma na nufin, amshi da akan yi a qarshen xangayen waqa. Ke nan ba wata aba ba ce cafiya illa wani gajeren amshi da kan zo a qarshen wasu xangaye na baiti ko baitocin waqa.

## Nau'o'in Cafiya

Dangane da xan nazarin da aka yi na wasu waqoqin da suke da irin wannan salo na amshi an fahimci cewa za a iya raba nau'o'in cafiya zuwa uku: gajeriyar cafiya da doguwar cafiya da kuma tagwan cafiya.

## Gajeriyar Cafiya

Ita irin wannan cafiya ba ta wuce kalma xaya rak. Ma'ana, abin da ake faxa a qarshen xango ba ya wuce kalma kwaya xaya. Ibrahim Lalula ya yi amfani da irin wannan cafiya a waqarsa ta begen Fatima. Duba waxannan baitoci da ke qasa:

Amshi: Sannu 'yar ma'aiki
Fatima Zahra'u mai tsarkin asali.

Bayarwa: "Da farko da sunnan Allah zan fara wanga waqe,
Cafiya: Fatima

Bayarwa: Shi yake kome ba mai ce da shi bari sake,
Cafiya: Fatima

Bayarwa: Ka san matsalata ya Allah ka ce mata warke,
Cafiya: Fatima

Bayarwa: Idan zai yi komai kumfa yakunu zai ce a take,
Cafiya: Fatima

Bayarwa: Ka amsa addu'ata rabbi domin Rasulu xan asalin asali.
Amshi: ...............................................................................................

Bayarwa: Kai salati ya Allah gun Abbul Falima,
Cafiya: Fatima

Bayarwa: Adadin sonka da shi adadin da shi ma yake ma,
Cafiya: Fatima

Bayarwa: Wa alihi 'ya'yan sayyadina Ali da Fatima,
Cafiya: Fatima

Bayarwa: Har da sahabbai ustapha ba ya rama,
Cafiya: Fatima son su da M
Bayarwa: A gaishe da Shehu Barhama mai tsarkin asali".
Amshi: ..................................................................................
(Ibrahim Lalula: Waqar Fatima bt. Na 1-2)

Uzairu Badamasi da Musa Gumel sun yi amfani da irin wannan nau'i na cafiya. Duba waxannan baitoci da ke qasa:

Amshi: Muhammadu Ture ya ce, mai makirci ya makara,
Wanda ya yi barci da yawa, ba ya jin kukan zakara,
Mu faxa ko kar mu faxi?
Mu fasa kowa ya sani.
"yahudu a shir xinku, qasarmu akwai Hizibullahi,

Cafiya: Qwarai

Bayarwa: Mun ba da jinananmu domin a tsare dinillahi,
Cafiya: Qwarai

Bayarwa: Kuma za ku yi mamakinmu idan muka taso wallahi,
Cafiya: Qwarai

Bayarwa: Duk da kun barci da yawa, ba kwa jin kukan zakara.
Wata rana za ku faxi
Amshi: ..............................................................................

Bayarwa: Su sace shanunmu Yahudu su nuna Fulani ne,
Cafiya: Qwarai

Bayarwa: Su xana bom a tasha su ce, 'yan boko haramun ne,
Cafiya: Qwarai

Bayarwa: Sun sace mata yanzu sun ce wai sojoji ne,
Cafiya: Qwarai

Bayarwa: Nufinsu a hau rigima da tallakka da sojoji a kara,
Wata rana za ku faxi.
Amshi: ..............................................................................
(Uzairu Badamasi: waqar mai makirci ya makara, bt. na 1-2).

Shi ma Musa Gumel ba a Bar shi a baya ba, wajen amfani irin wannan cafiya.
Duba baitin da aka kawo a qasa:

Amshi: Sannu Mazan Fama,
In na ga xakinka,
Tausayi na kama ni,
Tuzuru.

Bayarwa: "Ni na xau guduma, na yinqura zan fasa kwai duba,
Cafiya: Tuzuru

Bayarwa: Fankilu aya ce tana nan ai ba a shafe ba,
Cafiya: Tuzuru

Bayarwa: Kamar fi'ili amri a ayar ko ba shi ne ba,
Cafiya: Tuzuru

Bayarwa: Ku tashi mu dudduba, hani ta yi wai shin ko horo.
Amshi: ..........................................................................

Bayarwa: Aure albarka ne, Malam gara ka tantance,
Cafiya: Tuzuru

Bayarwa: Ka daina yin shakka, ta Annabi ko a cikin zance,
Cafiya: Tuzuru

Bayarwa: Ka rushe tsarinka, ka bi Annabi sai ka iyo dace,
Cafiya: Tuzuru

Bayarwa: Tun da ka qyale shi, tuzuru dole ka susuce a soro.
Amshi: ..............................................................................
(Musa Gumel: waqar Mazan Fama (Tuzuru), bt. na 3-4).

Idan aka lura da baitocin da aka kawa a sama za a ga cafiyar da ke zuwa a qarshen xangayensu, ba ta wuce kalma xaya. Ganin haka sai aka yi wa wannan cafiya laqabi da gajeriyar cafiya.

**Doguwar Cafiya**

Ita kuma, irin wannan cafiya ta qunshi kalmomi da yawa. Ta fara daga kan kalmomi biyu zuwa sama da haka. Wato kalmomin da ake faxa a qarshen xango sun wuce kalma xaya. Duba waxannan misalai da ke qasa:

Amshi: Dole mu tashi mu jinjina maka,
Bello ziyararka mun yaba ta,
Ba ya nisa garin masoyi,
Ka xaga tuta yau ta qauna,
Aikin da rago ba zai iya ba.
Bayarwa: "Ilahu gwanin hikima na gode, maka mai qulla qauna cikin zukata.
Cafiya: Ai haka soyayya ta gada

Bayarwa: Salli ala habibinka, manzo Annabi Shugaban masu bauta
Cafiya: Ai haka soyayya ta gada

Bayarwa: Ka sa da xiya na gida ma'aiki irin su Batula da Zuriyarta,
Cafiya: Ai haka soyayya ta gada

Bayarwa: Wanda ya bi su saboda qauna, ina da yakini ba zai vace ba.
Amshi: ..............................................................................

Bayarwa: Ai ni sai yanzu na yarda, da ba ya nisa garin masoyi,
Cafiya: Ai haka soyayya ta gada

Bayarwa: In na tuno nisan Kano zuwa ga Legas mamaki nake yi,
Cafiya: Ai haka soyayya ta gada

Bayarwa: Amma shi Bello saboda qauna, ya ce zai zo shi in yo tsimayi,
Cafiya: Ai haka soyayya ta gada

Bayarwa: Abinka da xan manyan mutane, ba ya alqawar bai cika ba".
Amshi: ........................................................................................................
(Musa Gumel: Waqar Ba ya nisa Garin Masoyi, bt. na 1-2)

Haka shi ma Kamilu a waqarsa da ya yi wa Baba Machina xan Majalisar wakilai ya yi amfani da irin wannan cafiya mai kalmomi da yawa. Duba waxannan baitoci da ke qasa:

Amshi: Gwanin wani bai yi ya gwarzona ba,
Takanxa bai fi rake zaqi ba,
Baba na Machina mun gode maka,
Ref ka lura da mu talakawa.
"da farko mai sama Allah shi ne masanin manufata.

Bayarwa: Da farko mai sama shi ne masanin manufata,

Cafiya: Baba na Machin kowa ya bi.

Bayarwa: Sarki mai duka shi ya yi mu maza, shi ya yi mata,
Cafiya: Baba na Machin kowa ya bi.

Bayarwa: Sarki mai sama shi ya yi Xankwairo, sannan mai sama ya yi yo Shata,
Cafiya: Baba na Machin kowa ya bi.

Bayarwa: Alhakim ya yi yo Alhaji Sarkin Taushi, mawaqa ne duka 'ya'yan baiwa".
Amshi: ................................................................................................

Bayarwa: Baba na Machina in ya zarce zai tura mu muje makaranta,
Cafiya: Baba na Machin kowa ya bi.

Bayarwa: Har ilimi zai bayar kyauta don miqa shi ga 'ya'ya mata,
Cafiya: Baba na Machin kowa ya bi.

Bayarwa: Ga inji kuma keken xinki za a raba shi ga 'ya'ya mata,
Cafiya: Baba na Machin kowa ya bi.

Bayarwa: Alhaji Baba Gwani na kamjir mun gode maka mu talakawa".
Amshi: ........................................................................................................
(Kamilu: waqar Baba na Machina kowa ya bi, bt. na 1-2).

Su kuma waxannan baitoci da aka kawo a sama, idan aka yi nazarin su da kyau za a ga cafiyar da kan zo a qarshen xangayen baitocin sun qunshi kalmomi da yawa ba kalma xaya ba. Don haka aka yi mata laqabi da doguwar cafiya.

**Tagwan Cafiya**

Irin wannan cafiya takan kasance iri biyu ko fiye a xangwayen da ke cikin baiti. Wato cafiyar da ke xango na farko takan bambanta da ta xango na biyu. Za a iya samun misalin wannan cafiya a waqar Kamilu da ya yi wa Malam Ibrahim Oska Shuaban karamar hukumar Nguru. Duba waxannan baitoci da ke qasa:

Amshi: Malam Ibrahim Oska,
Guru za mu sha mamaki
Matsayin da duk aka ba shi,
Gwarzonmu ya cancanta.

Bayarwa: "To 'yan uwa ku jiya, na sake buxe taska.
Cafiya: Malam Ibrahim Oska

Bayarwa: Xan Garba angon, Ummi almajiri mai waqa,
Cafiya: Guru za mu sha mamaki

Bayarwa: Na zo in ba ku bayani, na faxe shi saqa-saqa,
Cafiya: Malam Ibrahim Oska

Bayarwa: A wajen bayanin waqa xan Garba ba na sata.
Amshi: ................................................................

Bayarwa: Komai riqa a siyasa kowa akwai Oganshi,
Cafiya: Malam Ibrahim Oska

Bayarwa: Haka duk tsiyar mai waqa shi ma akwai Oganshi,
Cafiya: Guru za mu sha mamaki

Bayarwa: Mu Oska ne Oganmu mun tabbata wallahi,
\Cafiya: Malam Ibrahim Oska

Bayarwa: Kome na faxa al'umma kowa ya rinqa fahimta"
Amshi: .......................................................................
(Kamilu Hussaini Xan Almajirin mawaqa: waqar Ibrahim Oska, bt. na 4-5).

Haka kuma a waqarsa ta Lawan Zulu ya sake amfani da irin wannan nau'i na cafiya. Duba waxannan baitoci da ke qasa:

Amshi: Jaki bai fi rago ba,
Har idan daraja ake nema,
Lawan Zulu ke godiya,
A wurin Allah mafi grima.
Bayarwa: "Ya ya waqa Lawan Zulu zan yi ban ji kuna ta tafi ba,
Cafiya: Jaki bai fi rago ba

Bayarwa: Ko ku a ganinku waqar da nai masa ba ta birge ku sosai ba,
Cafiya: Har idan daraja ake nema

Bayarwa: Idan dai har ina raye, wannan ba ita ce ta qarshe ba,
Cafiya: Jaki bai fi rago

Bayarwa: A nan gaba dole zan masa waqa, ba waqa ta wasa ba.
Amshi: ...............................................................................

Bayarwa: Tun da ga mai gaskiya, ba za mu bi dillali macuta ba,
Cafiya: Jaki bai fi rago

Bayarwa: Idan kun dubi hebur da kyau, ba ludan miya ne ba,
Cafiya: Har idan daraja ake nema.

Bayarwa: Agwagwa na fahimce ta tabbas, ba tsafta ta gada ba,
Cafiya: Jaki bai fi rago

Bayarwa: Makaho idan ya ce ku yi jifa, ba ka san me ya taka ba.
Amshi: ......................................................................................
(Kamilu Hussaini: Waqar Jaki ba fi raga ba, bt. na 1-2)

Shi ma Abdullah Alfazazy ya yi amfani da irin wannan nau'i na cafiya a waqar da ya yi wa major Almustapha. Duba waxannan baitoci da ke qasa:

Amshi: Mu dai murna muke,
Major Hamza Almustapha a yau ya dawo
Mu yi masa marhaba,
Lale-lale yau gaskiya tai rana.
Bayarwa: "Ni da sunan rabbana wanda shi ke juyan zamani
Cafiya: Sarkina

Bayarwa: Mai kyauta Qadirin shi ke bayarwa yai hani,
Cafiya: Sarkina

Bayarwa: Ilahi ka kara tsira ga wanda nake so in gani
Cafiya: Manzona

Bayarwa: Ni dai kan saka har sahabai su na rike su zama gatana.
Amshi: ....................................................................................
(Abdullah Alfa Zazy: waqar Almustapha, bt. na 1)

Idan aka duba cafiya da ke zuwa a qarshen xangwaye na waxannan baitocin da aka kawo a sama za a ga cafiyar da ake yi a qarshen xango na farkon baiti ba ita ba ce a qarshen xango na biyu wannan baiti. A nan an samu cafiya iri biyu ta farkon xangon baiti da kuma ta biyun xango na wannan baiti wadda kalmominta, suka bambanta da ta farko xango wannan ne ya sa aka kira irin wannan nau'i na cafiya tagwan cafiya.

## Yanaye-yanayen Cafiya

Cafiya tana da yanayi iri-iri. Amma yawanci tushenta daga amshi yake fitowa. Ma'ana, mafi akasarin cafiya ana ciro ta ne daga amshi waqa. Misali: idan aka duba waqoqin da aka kawo a wannan maqala za a iya tabbatar da haka. Duba waqar Begen Fatima ta Ibrahim Lalula da waqar Mazan Fama ta Musa Gumel da waqar Uzairu Badamasi ta Varawon 'Yan Mata da waqar Ibrahim Oska ta Kamilu Hussaini duk za a ga tushen cafiyarsu an ciro shi ne daga amshin waqoqin.

Sai dai kuma duk da cewa tushen cafiya yawanci yana kasancewa ne daga amshi, amma a wasu lokuta akan samu cafiya wadda tushenta sam ba daga amshi yake ba. Duba wxannan baitoci da ke qasa:

Amshi: Muhammadu Ture ya ce,
Mai makirci ya makara,
Wanda ya yi barci da yawa,
Ba ya jin kukan zakara,
Mu faxa ko kar mu faxi?
Mu fasa kowa ya sani.

Bayarwa: "Yahudu a shir xinku qasarmu akwai Hizibullahi,
Cafiya: Qwarai

Bayarwa: Mun ba da jinananmu domin a tsare dinillahi,
Cafiya: Qwarai

Bayarwa: Kuma za ku yi mamakinmu idan muka taso wallahi,
Cafiya: Qwarai

Bayarwa: Duk da kun barci da yawa ba kwa jin kukan zakara,
Wata rana za ku faxi".
Amshi: ...................................................................................................
(Uzairu Badamasi: waqar mai makirci ya makara, bt. na 1).

Idan aka duba cafiyar da ke cikin wannan baiti za a ga babu ita a cikin amshin waqar. Wannan ya nuna cewa ba kowace cafiya ba ce tushenta yake kasancewa daga amshin waqa.

Shi ma kamilu ya yi amfani da irin wannan cafiya. Duba wannan baiti da ke qasa:

Amshi: Mu P.D.P duka ta kashe mu,
Ni ma haka Kamilu ta kashe ni,
Dubban jama'a duka sun guje mata,
Don ba su tsira da ko kwabo ba.

Bayarwa: "Sarki Allah msanin zukatanmu, shi zai tsare min lafiyata,
Cafiya: ku bar ta kwai rigar qaya ce

Bayarwa: Na roqi tabaraka wahidin, sarki ka daxa min hattara ta,
Cafiya: Kubar ta kawai rigar qaya ce

Bayarwa: Tabbas mun yarda da xan Amina, fiyayyen Annabi xan Suwaiba".
Amshi: ...........................................................................................................
(Kamilu Hussaini: waqar P.D.P Rigar Qaya ce: bt na 1)

Ita ma wannan cafiya idan aka duba cikin amshin waqar, za a ga babu ita.

Sannan akwai cafiya mai falan xaya. Wato wadda abin da ake faxa a qarshen xango ba ya canzawa har qarshen waqa. Waqar Begen Fatima da aka kawo misali da ita a sama, ta Ibrahim Lalula da waqar Sannu Mazan Fama ta Musa Gumel duk suna da irin wannan yanayi, saboda kalmomin cafiyar ba sa canzawa har qarshen waqar.

Haka kuma, akan sami cafiya mai sirki, wato wadda akan samu bambancin cafiya a tsakanin wasu baitoci da ke cikin waqar. Duba waxannan baitoci da ke qasa:

Bayarwa: "Ubangiji Allah dafa mana za mu tsare hakki
Cafiya: 'yan mata

Bayarwa: Za mu buga a buga a bisa haka mun yi shirin yaqi,
Cafiya: 'yan mata

Bayarwa: Tsira da aminci gun nasirul hakki bil hakki,
Cafiya: ‘yan mata

Bayarwa: Da alihi Allah shi ne asalin tsare hakkin ‘yan mata.
Amshi: Lafiya babu Dujal na Abuja na satar ‘yan mata

Bayarwa: Da gwamnatin Landon da America sun haxa baqinsu,
Cafiya: ‘Yan banza

Bayarwa: Israila ta ba su saqo sun bai wa yaransu
Cafiya: ‘Yan banza

Bayarwa: Sun kashe jama’a sun zo sun sace ‘ya’yansu,
Cafiya: ‘Yan banza

Bayarwa: Fir’auna suke koyi sun kau da maza suna voye ‘yan mata”.
Amshi: ..............................................................................................
(Uzairu Badamasi: Waqar Varawon ‘yan mata, bt. na 1 da 3)

Haka shi wannan yanayi na cafiya an same shi a waqar Hamza Almustapha ta Abdullah Alfazazy. Duba wannan misali da ke qasa:

Bayarwa: “Da farko sallama ce nake yi wa duka al’umma,
Cafiya: ya dawo

Bayarwa: Sai ku saurare ni ga baituka zan yi kuji kuma,
Cafiya: ya dawo

Bayarwa: Kan batun Almustapha Hamza Majon nan shi zan yi fa,
Cafiya: ya dawo

Bayarwa: Zan sanar muku ya dawo ba wata tantama ‘yan uwana:
Amshi: .....................................................................

Bayarwa: Su komai suka tambaya, Hamza zai amsa musu
Cafiya: Lallai

Bayarwa: Sam ba wata gardama
Cafiya: Lallai

Bayarwa: Hujja zai kawo musu
Cafiya: Lallai

Bayarwa: Sheda zai kawo musu
Cafiya: Lallai

Bayarwa: A fili har haxa
Cafiya: Lallai

Bayarwa: Jama’a sun hallara
Cafiya: Lallai

Bayarwa: Kowa a kotu yana gurin

Cafiya: Lallai

Bayarwa: Hujja tasa sai ya zama kowowa
Cafiya: Lallai

Bayarwa: Sai jama'a suna tafawa har wasu suna kuka".
Amshi: ...........................................................................
(Abdullah Alfa Zazy: Waqar Almustapha, bt. na 2 da 6)

Idan aka lura da waxannan baitoci guda biyu da aka kawo a sama, za a ga cafiya da take a baiti na farko ta bambanta da wadda take baiti na biyu.

## Muhimmancin Cafiya

Cafiya tana da matuqar muhimmanci kwarai da gaske wajen mawaqan zamani. Domin sukan yi amfani da ita wajen qarfafa maganar da suka faxa a cikin xango na baiti. Duba wannan baitin da ke qasa:

Bayarwa: "Allahu na godewa, don hikimarsa ce da nufinsa
Cafiya: Lalle

Bayarwa: Waqar da na yi ta hantsi, in ka ji baitikan da ta qunsa,
Cafiya: Lalle

Bayarwa: Kai ma za ka zamto shaida, akwai wata albishir ga matasa,
Cafiya: Lalle

Bayarwa: Yau ga ni ga ku samari, waqar taku ce a taqaice".
Amshi: ...........................................................................................
(Musa Gumel: Waqar Albishrin ku Matasa, bt. na 1).

Haka kuma, takan qara wa waqa armashi ta qawata ta. Sannan takan ja hankalin masu sauraro zuwa ga manufa. Muhimmancin bai tsaya a nan ba, domin takan saka wa masu sauraron karsashi da annashuwa.

## Kammalawa

A wannan bincike da aka gudanar an nazarci wani salon amshi ne da aka yi wa laqabi da *Cafiya*, a wasu waqoqi guda tara na mawaqa daban-daban. A binciken an gano nau'in *Cafiya* har guda uku da suka haxa da: doguwar cafiya da gajeriyar cafiyar da tagwan *Cafiya*. Sannan binciken ya fito da wasu yanye-yanaye da ita wannan *Cafiya* take da su. Haka kuma, an gano cewa cafiya tana da muhimmanci a wajen mawaqa ta fuskoki da dama da suka haxa da: qarfafa maganar da ke cikin xango na baiti da qawata waqa da jawo hankalin masu sauraro zuwa ga manufa da saka musu karsashi da annashuwa.

## Manazarta

Abba, M. da Zulyadaini, B. (2000). *Nazari Kan Waqar Baka Ta Hausa*. Zaria: Gaskiya Corporation Ltd.

Bello, G. (1976). "Yabo, Zuga da Zambo a Waqoqin Sarauta" a Cikin *Harsunan Nijeriya VI* Kano: Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, jami'ar Bayero.

Bergery, G. P. (1951). *A Hausa-English Dictionary and Englsh-Hausa Vocabulary*. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited.

Bunza, A. M. (2009). *Narambaxa*. Lagos: Ibrash Islamic Publication Centre.

CNHN, (2006). *Qamusun Hausa Na Jami'ar Bayero.* Kano: Wallafa Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya,Jami'ar Bayero.

Xangambo, A. (1981). "Rikixar Azanci: Siddibarun Salo da Harshe a Cikin Tabarqoqo" Tahamisin Aliyu xan Sidi a Cikin *Studies in Hausa Language, Literature and Culture.* Kano: Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, jami'ar Bayero.

Gusau, S. M. (2003). Jagoran Nazarin Waqar Baka. Abuja: Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S. M. (2008). *Waqoqin Baka A Qasar Hausa: Sigoginsu Da Yanaye Yanayensu*. Kano: Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S.M. (1985). "Salo da Sarrafa Harshe a Waqoqin Baka na Hausa" a Cikin *Nazari a Kan Harshe da Adabi da Al'adu na Hausa III*. Kano. Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, jami'ar Bayero.

Gusau, S.M. (1985). "Waqar Gogarmar Tudu ta Ibrahim Narambaxa a Mazubin Nazari" a Cikin *Algaita: Journal of Current Research in Hausa Studies*. Vol.1 . No.1 Kano. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, jami'ar Bayero.

Gusau, S. M. (2014). *Waqar Baka Bahaushiya*. Kano: Bayero University, Inaugural Lecture Series No. 14.

Muhammad, D. ed (1990). *Hausa Metalanguage/Qamus Na Kevavvun Kalmomi*. Ibadan: University Press Limited.

Schuh, R.G. (2002). "Karin Waqoqin Aure na Xanmaraya Jos" a Cikin *Studies in Hausa Language, Literature and Culture* (The Fifth International Conference). Kano: Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Yahya, A. B. (2016). *Salo Asirin Waqa*. Sokoto: Guaranty Printers.

**Hira da Mawaqa**

Suna: Musa Sani Zakari (Musa Gumel)
Unguwa: Hausari ward, Nguru, Yobe state.

Suna: Ibrahim Bn Ishaq (Ibrahim Lalula)
Unguwa: Hausari ward, Nguru, Yobe state.

Suna: Ahmad Alhaji Abdurrahman (Ahmad Kano)
Unguwa: Unguwar Sarkin Hausawa, Gashuwa, Yobe State.

Suna: Abubakar Malam Ya'u (Abubakar Suwa'ilu)
Unguwa: Bulabulin Ward, Nguru, Yobe State.